# Tasirin Zamani A Kan Tattalin Arziqin Hausawa Bincike A Kan Sana'ar Qira

**AHMED ALIYU (Ph.D)**
ahmedaliyuturaki@gmail.com
08065402292
Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kwalejin Ilimi Da Harkokin Shari'a Ta Yusuf Bala Usman, Daura.

**Da**

**SANI ALIYU**
Sanialiyu101@gmail.com
08039299012
Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Tarayya, Dutsinma, Jihar Katsina
Yuni, 2024

## Tsakure

*Al'ummar Hausawa, al'umma ce wadda ta ratso zanguna mabambanta na zamantakewar rayuwa, sun samu canje-canje da dama a sanadiyar cuxanya da wasu al'ummomi da kuma sauyin zamani.Kaxan daga cikin canjin harda na sana'o'insu da suke dogara a kansu. Don sukan ce, "Sana'a sa'a, rashin sana'a sata". Haqiqa! Sana'ao'in Hausawa cike suke da muhimmanci da martaba qwarai da gaske, domin da ita suka dogara, kuma ita ce qashin bayan tattalin arziqinsu. Rayuwarsu kacokan ta ta'allaqa ne a kan irin waxannan sana'o'in musamman da rani, domin a lokacin damina kowa manomi ne maza da mata, yaro da babba. Don haka ne, manyan sana'o'in masu qima ne da alfanu da babu yadda rayuwa za ta yiwu ba tare da su ba, domin kowane gurbin da za su bari, givin ba zai ciku ba, wanda dole sai da su. Sai dai kash! yadda ake yin su a da ba haka suke a yanzu ba, dalilin canje-canje da suka samu, daga cikin sana'o'in sun haxa da Sassaqa da Saqa da Dukanci da Fawa da Su da Rini da kuma sana'ar qira. Wannan takarda ta yi bayani ne a kan ma'anar Sana'a da Qira, kayan aikinta da rabe-rabenta,sannan ta tsakuro kaxan daga cikin kayan da sana'ar ke samarwa, haka kuma ta kawo canje-canje da sana'ar ta samu, binciken ya karkarta ne kacokam akan sana'ar qira.*

## Gabatarwa

Canji shi ne sauyi da ake samu na wani al'amari da aka san yadda yake a asalinsa, wannan canji kan faru a cikin tsarin zamantakewar ko tattalin arziqi ko siyasa ko xabi'a. Abubuwan da ke kawo canji kuwa su ne sababbin buqatun rayuwa da matsalolin yau da kullum. A dalilin biyan buqatun rayuwa da neman warware matsaloli na rayuwa, canje-canje su shigo, wannan ci gaba ne. Ado, (NLH 83 2015). Lokacin da mutane suka fara noma ba su da kayan aiki, da hannu ake yi, da aka fara ci gaba sai suka gane dabarar feqe vangarorin duwatsu, su yi waxansu da faxi-faxi, waxansu da tsini-tsini, don su huta sa yatsunsu. Suna qara gyara kayan aikinsu, ana nan har waxansu daga cikinsu suka zama gwanayen qera abubuwa daban-

daban. Qira ta samu ke nan a cikin sana'o'in Hausawa. Daga nan sai fita farauta ta yi sauqi, wato da kaka, qira ta zama sana'a babba bayan noma, wasu suka koyi saqa wasu kuma kwava yimbu suna gina tukane, wasu sassaqa domin samun abin masarufi, (Rimmer, 1966: 42).

Saboda haka, wannan takarda ba ta yi tuya ta manta da albasa ba, domin ta qyallaro irin canje-canje da aka samu a vangaran sana'ar qira, kayayyakin da take samarwa wajen bunqasar sauran sana'o'i da kuma ire-iren kayan gudanar da sana'ar, domin raba zare da abawa, takardar ta leqo jiya da kuma yau domin ganin irin wainar da ake toyawa.

**1.1 Ra'in Bincike**

Sababbin buqatun rayuwa da matsalolin yau da kullum su ne ke kawo canje-canjen al'adun al'umma. Bincike ya tabbatar akwai ra'o'i da suka yi magana a kan ci gaba da bunqasar da al'umma ke samu a fannoni da dama, a zamantakewa na rayuwa, daga ciki harda wanda ya yi magana a kan Ra'in canje-canjen tattalin arqin al'umma (Economic (Mandan) Theory of Social Change) masanin da ya yi qaurin suna wajen wannan ra'i ba bu kamar Karl Marx. Abin nufi shi ne, duk abin da ya wanzu, ya samu ne a sanadiyar kayayyakin duniya waxanda sukan bunqasa. Don haka aka xora wannan takarda a bisa wannan ra'i, ganin yadda abubuwa ke bunqasa sanadiyar cuxanya tsakanin al'ummomi guda biyu, ke nan akwai canji ga al'adun Hausawa musamman sana'o'i, sakamakon cuxanya da wasu al'ummu, misali Larabawa da Turawa da sauransu.

**2.0 Ma'anar Sana'**

Sana'a wata hanya ce da xan-Adam kan ta'allaqa a kanta domin samun abin masarufi, wadda ta shafi sha'anin kasuwanci, wato sha'anin saye da sayarwa. Ga Bahaushe, sana'a ita ce qashin bayan tattalin arziqinsa. (Xan'iya, 2006:1).

Garba, (1991:1) ya bayyana sana'a da cewar ita ce ginshiqin rayuwa da tattalin arziqin yau da kullun na Hausawa, tare kuma da manyan hanyoyin gano martabar mutum da kuma qasaitarsa da matsayinsa cikin al'umma. Baya ga noma da yake ruwan dare, Hausawa na qara wa kansu wata sana'a domin samun abinci a lokacin rani.

Haka nan Madabo (1976:9) a ra'ayinsa ya bayyana sana'a a matsayin daxaxxiyar al`ada da ta nuna Hausawa a idon duniya, ta kuma bunqasa qasar Hausa ta yadda baqi suke zaune cikin jin daxi sakamakon sana'o'i daban-daban. Ita ko ba a yinta sai da wuta, don haka masu hikima cewa "Ana zaton wuta a maqera sai ka same ta a masaqa".

Don haka, masana sun yi qoqarin tsara sana'o'in Hausawa bisa kashi uku dangane da ra'ayinsu da fahimtarsu.

Yahaya da Xangambo (1986:173-174) sun raba sana'o'in zuwa gida uku. Sana'ar noma da sana'ar sarrafa wani abu domin samar da wani abun. Misali sana'ar qarfe- qira, zare- saqa, fata- dukanci da sauransu. Sai sana'ar sarrafa jari da qwarewa misali: kasuwanci, gini da saqa da sauransu.

A nan, muna iya kallon sana'a na a matsayin hanya ta amfani da azanci da hikima ta sarrafa albarkatu da ni'imomin da xan-Adam ya mallaka don buqatun yau da kullum, kuma hanyar dogaro domin samun biyan buqatu na yau da kullum a cikin rayuwar xan-Adam.

Don haka, bisa qa'idojin al`adun Hausawa, ba kowace sana'a kowa yake yi ba, a'a, kowace da mai yinta, waxansu na mata ne, waxansu na maza ne, waxansu kuma suna yi ne a tare ma'ana kowanne jinsi zai iya gudanar da sana'ar.

**Misali**:

| **Maza** | **Mata** | **Tarayya** |
|---|---|---|
| Jima | Kitso | Saqa |
| Dukanci | Dakau | Dillanci |
| Rini | Sussuka | Aikatau |
| Wanzanci | Dafe-dafe | Qirar (farfaru) |
| Fawa | | Roqo |
| Qirar(babbaqu) | | |

Da dai sauran su (Yahaya, 1986:173).

### 3.0 Ma'anar Qira

Masana da dama sun tofa albarkacin bakinsu akan abin da ake nufi da qira. Galadanci da wasu (1992:92) sun bayyana qira a matsayin "Sana'ar sarrafa qarfe don samar da wasu abubuwan amfani".

Qira sana'a ce ta fasahar sarrafa qarfe da ke da alaqa qut-da-qut da wasu fitattun sana'o'i a qasar Hausa. Masu wannan sana'a su ake kira Maqera. Qira aiki ne na sarrafa qarfe a mai da shi makami, ko ma'aikaci da dai sauransu. Ana narka qarfe ko tama ko azurfa ko zinari, a mayar da ita wani abin amfani. Kayan qira kuwa su ne kamar zuga-zugi da uwar maqera da guduma da masaba da salleta da awartaki da sauransu, (Alhassan,1982: 52). Sallau, (2010:21) Ya ce "Qira sana'a ce da aka fi yi lokacin rani domin tanadar kayan aikin noma, amma duk da haka ana yin ta kowane lokaci na shekara domin samar da kayan amfanin gida na yau da kullum".

Kenan, za a iya kallon qira a matsayin fasaha, sana'a ta sarrafa qarfe domin samarwa al'umma wasu kayayyyakin aiki domin biyan buqatunsu na yau da kullum, a gida ko daji, ko na kare kai. Masu wannan sana'a, su ake kira maqera. Maqera sun kasu kashi biyu, kamar yadda, Brob da Baba, (1996:22) da Aliyu, A.(2010:) suka tabbatar.

- Maqeran babbaqu (smithery)
- Maqeran farfaru (casting)

**Maqeran Babbaqu**: - waxannan maqera su ne masu fasahar amfani da baqin qarfe wajen gudanar da sana'arsu, su ne ke qera kayan noman Hausawa irinsu fartanya, garma, magirbi da kuma kayan yaqi irinsu takobi da mashi da kibiya da qyaure da sauransu, kuma sune na jama'a.

**Maqeran Farfaru**: - wannan maqera kuwa suna fasahar amfani da farin qarfe. Maqeran farin qarfe su aka fi sani da qera kayan adon mata na alatu, kamar mundaye da ‘yankunne, zobe da awarwaro da taron hanci da murjani da kuma kayan adon doki na sirdi da likkafa da sauransu.
Maqeran sun kasu biyu, da maqeran baqi da na fari. Maqeran baqi su ne masu aiki da baqin qarfe kawai, su ke qera dukkan kayan noma dana yaqi da na farauta da na sauran sana’o’i, (Alhasan,1982:53).

Maqeran fari kuwa, su ne masu fasahar aiki da waxansu irin qarafa, kamar su azurfa da goran ruwa. Da su ake qera qananan kaya irin na adon mata, da kayan dawaki.
Maqeran baqin qarfe kan yi wa kansu kirari da cewa:

> “Sai ni baqi, dodon qarfe
> Mai amana da maharba!
> Sai ni na kaka gwani, ni na iya don kaina!
> Da ba domin taya ba, da na yi mota!
> Ba dan ni ba, da qasa ta yi saura!
> Kai ba don ni ba, da maza sun yi gizo!
> Sai ni na Ali, gatan kaka, mai abin mamaki!
> Qarya kuke, magauta.
> Sai na gaji na bari dan kaina” (Rimmer, 1968: 118)

A nan idan muka dubi wannan kirari, za mu ga irin yadda wannan fasahar ta qira ke samar da kayan aiki ga wata sana’ar. Misali inda aka kawo cewa “Ba don ni ba da qasa ta yi saura, kuma da maza sun yi gizo” wato sana’r na samar da kayan noma da na aski.

## 4.0 Yadda Ake Sana’ar Qira a da

Hausawa na cewa “Ba a cin ‘ya’yan itace daga sama”. Don haka, yana da kyau kafin aga yadda ake qira, mu waiga ga kayan qiran domin an ce “waiwaye adon tafiya” (Koko,2011:4).

Maqera kan buqaci kayayyakin domin aiwatar da sana’ar ta su, muhimmai daga ciki sun haxa da: Uwar maqera da masaba da matsoni da gawayi da sauransu, (Maxauci,1968:59).

- Uwar maqera - qarfe ne mai faxin kai da yake a kafe, a kansa ake xora qarfe a buga.
- Zuga-zugi - da shi ake rura wutar qira, jaka-jakar fata ce.
- Gawayi- shi ake sawa a samar da wuta.
- Masaba- qarfe ne dunqulalle da ake dukan qarfe da aka fito da shi daga wuta.
- Awartaki - shi ne maqeri ke sa qarfe a wuta, da kuma ciro shi in ya yi ja, ya riqe ya buga.
- Muntalaga - qaramar guduma mai qotar itace.
- Bakin qira - rarakakken abu ne da ake da qasa wanda a ke cusa qofofin zuga-zugi a ciki.
- Madoshi - qarfe ne mai tsini da ake sawa a wuta domin a huda qota da shi.
- Magagari - qarfe ne mai faxi da tsawo, yana da kaushi wanda ake koxa ko kaifafa abunda aka qera.
- Qarfe – wanda a ake sawa a wuta a sarrafa domin samar da ma’aikaci.
- Matoni – dogon qarfe mai qota, maqera na tona cikin gawayi da iza wuta.
- Maqera – wurin yin qira.

- Dutsi/kaskon maqera – mazubin ruwa a gefen maqeri. Da dai sauransu, (Aliyu, 2010: 25-32).

Kamar yadda Hausawa ke cewa "Abun da yawa wai mutuwa ta je kasuwa" za mu xauki abu xaya cikin kayan da maqera suke qerawa muga yadda ake gudanar da shi, wannan kuwa ita ce Fartanya.

Abubuwa da ake buqata wajan yin fasahar qera fartanya sun haxa da, qarfen yin ruwan da qota ta ice. Shirin wutar maqera ya haxa da gawayi dan haxa wutar qira, zuga-zugi don hura wutar da kayan aiki kamar su awartaki da uwar maqera da guduma da dai sauran su, (Hira da maqera, Yuni 2015).

Bayan an samo qarfen yin ruwan fartanya, sai a saka shi cikin wuta a yi ta zuga, har sai ya yi ja, yadda za a iya lauya shi. Da ya gama ja sai a xauko shi da awartaki a xora shi bisa uwar maqera, sannan a buga shi yadda ake so ya zama. Sai a cigaba da haka, har a fitar da sigar ruwan fartanya, daga nan sai a yi amfani da masaba don a sa qarfe ya yi faxi da kaifi bayan an miqar da shi da guduma, kana sai asa magagari a goge shi don kaifin ya fito sosai. An gama qera ruwan fartanya ke nan. Daga nan sai a sa madoshi a wuta ya yi ja, sannan a huda qotar a sa ruwan, fartanya ta haxu kenan (Galadanci, 1992:93).

### 4.1 Ire-Iren Abubuwan Da Maqeran Babbaqu Ke Qerawa

**Na Gida: -** Wato wurin kwanciya ko hutawa.

| | Kalma | Ma'ana |
|---|---|---|
| i. | Adda - | Doguwar wuqa mai nauyi faffaxa da qota akan yi saran bishiya da ita kuma makami ce. |
| ii. | Aska/yar – tsagu | Qaramar wuqa mai kaifin gaske wadda wanzamai ke aski, ko kaciya ko cire beli. |
| iii. | Almakashi - | Maqera suke qera wa maxinka shi domin yanka yadi. |
| iv. | Basilla - | Qarfe kamar doguwar allura ana xinkin buhu da ita. |
| v. | Calii - | Maqushin yi wa jaki lautun kaya biyu a lokaci guda |
| vi. | Dagi - | Matoshin rijiya ko rami |
| vii. | Gatari - | Gatari saran bishiya ko yin faskare |
| viii. | Gizago - | Ma'aikacin sassaqa mai gajeriyar qota da qaramin ruwa |
| ix. | Hantsaki - | Qaramin qarfe mai gwafa abun cire qaya. |
| x. | Kura - | Gajeren qarfe mai maqatu na xauko guga a rijiya |
| xi. | Kartaji - | Wuqa mai qota ta wanke qwarya |
| xii. | Majuyi - | Qarfe mai tavavven baki da faxi na juya waina ko qosai |
| xiii. | Masassabi - | Ma'aikacin sarar qasa ko girbi |
| xiv. | Minjagara - | Ma'aikaci mai yatsu na shara |
| xv. | Turke - | Qarfe mai gwafa da ake bugawa qasa domin xaure dabba. |
| xvi. | Tsinke - | Qarfe mai tsini da qotar ice da dukawa ke amfani da shi ko mata masu tsefe kai. |
| xvii. | Wuqa - | Wuqa mai kaifi biyu. |
| xviii. | Zarto - | Mawashin wuqa ko fartanya da sauransu. |

| | | |
|---|---|---|
| xix. | Zobe - | Wanda ake sawa jikin ma'aikaci dan gudun kwavewa. |

**Na Daji: -** wato wurin neman abun biyan buqatu, abinci ko magani ko sutura, ko nama.

| | **Kalma** | **Ma'ana** |
|---|---|---|
| i. | Adda - | Doguwar wuqa mai nauyi faffaxa da qota akan yi saran bishiya da ita kuma makami ce. |
| ii. | Fartanya - | Wadda ake duqawa a yi noma. |
| iii. | Galma - | Wadda ake xora wa shanu su yi huxa. |
| iv. | Garma - | Mai gajeriyar qota da faffaxan ruwa ta huxa da hannu |
| v. | Gatari - | Gatari saran bishiya a daji ko itace. |
| vi. | Masassabi - | Ma'aikacin sassabe a gona ko yin girbi. |
| vii. | Minjagar - | Ma'aikaci mai yatsu da doguwar sanda ana yaye haki ko sharar goma da shi. |
| viii. | Lauje - | Lanqwasasshen qarfe da qota mai kaifi ana yanke hatsi ko kaba ko ciyawa. |
| ix. | Sungumi - | Ma'aikaci mai doguwar qota da rowan magirbi wanda ake saran ramin shuka daga tsaye. |

**Na Kare Kai -** wato kare kai daga abokan gaba ko namun daji.

| | **Kalma** | **Ma'ana** |
|---|---|---|
| i. | Adda - | Doguwar wuqa mai nauyi faffaxa da qota ta kare kai |
| ii. | Barandami - | Zabgegen qarfe mai lanqwasa domin yin faxa ko kare kai. |
| iii. | Kibiya - | Qarfe da ake sawa kara ko ice domin yin halbi daga nesa ko a saman Katanga maganin varayi. |
| iv. | Kuge - | Wani qarfe mai dungu uku, yana da qara, ana buga shi wajen yaqi. |
| v. | Qyaure - | Jibgegen qarfe da ake marfi da shi a qofar gari ko gida domin kariya daga abokan gaba. |
| vi. | Likkafa - | Qarfen da yake reto a gefen doki inda mahayin doki yakansa qafa. |
| vii. | Mashi - | Dogon qarfe mai tsini wanda ake sukar abokan gaba wajen yaqi. |
| viii. | Takobi - | Zungureriyar wuqa mai gwavi da kaifi biyu da mariqi da kube domin sara ko kare kai. |
| ix. | Wuqa - | Wuqa mai kaifi biyu cikin kube don kare kai. |

(Aliyu, 2010:25-33).

Waxannan misalai da suka gabata da sauran waxanda ba a sami dammar ambata ba, na daga cikin ire-iren abubuwan da maqeran babbaqu ke qerawa domin amfani a gida da daji da kuma kare kai. Don haka, Koko (2011:15) Ta kawo jerin Karin maganganu na kayan aiki, ciki harda masu alaqa da waxannan kaya da aka jero, ta ce,

"Guntun gatarinka ya fi sari ka ba ni,

Mun saba da faxuwar gaturra,
Xaxin wuqa baya kada gaban doki,
Ba a qwace wa yaro galma".

## 4.2 Abubuwan da Maqeran Farfaru ke Qerawa

Maqeran farfaru na samar da kayayyaki da dama ga jama'a musamman na kwalliya da kuma amfanin yau da kullum a cikin gida da kuma na kayan dawaki, ga kaxan daga ciki-

- **Kayan Kwalliya**-Akwai-'yankunne, awarwaro,taron hanci, 'yanhannu,zobba da kuma abun wuya da sauransu.
- **Kayan Amfani a gida-**Kaxan daga ciki akwai, cokulla da tukane da maburki da sauransu.
- **Kayan Dawaki**- kamar likkafa da lizzami da kuma kayan kwalliyar doki da sauransu, (Hira da Maqera).

## 5.0 Canje-canje da Sana'ar ta Samu a Yau

Kamar yadda Ado, (2014:20), ya bayyana cewa, canji na samuwa ne adalilin cuxanya. "A duk lokacin da aka samu cuxanya tsakanin wata qabila da wata, masna harshen Hausa, irin su Salim, (1986:2-3) da Zarruk (1986:12) sun yi bayani cewa dole ne a sami aro na harshe da al'ada. Hausawa na cewa, danqo ba ya faxuwa qasa banza, in bai xauki qasa ba ya xauki haki", Adamu (2005:41) ya tabbatar da hakan da ya ce "A duk lokacin da Bahaushe ya ci karo da wani abu sabo, nan-da-nan ya ke karvar sa, in har ya yi daidai da abin day a saba da shi". Don haka, sana'o'in Hausawa ma ba a barsu a baya ba, kaxan daga ciki akwai-

Qere-qeren zamani, kamar yadda Hausawa ke cewa "Zamani riga" wannan haka yake domin duk wanda ya qi sawa ya tafi ya barshi. Don haka, qerere na zamani sun yi tasiri qwarai da gaske a wajen kayan da maqeran babbaqu da farfaru ke samar wa al'umma na amfani gida da daji da kuma kare kai, misali. Na'urorin da injina ta fuskar noma da kayan sana'o'i waxanda ada maqera ke samar dasu, kamar su-

## 5.1 Kayan Amfanin Gida

- Kayan amfani cikin gida kamar, wuqaqe da tukane da basulla da cokulla, almakashi da sauransu. A da maqera na taka muhimmiyar rawa wajen samar da su, amma yanzu ina! Wannan an sami canji inda ake samar da su daga kamfuna.
- Kayan ado na mata na kamfani, maimakon wanda maqera ke yi, misali sarqar wuya, xan-hannu, zobba 'yankunne da dai sauransu. Wannan ya fara zama tarihi, yanzu akan samar da su kai tsaye da kamfani.
- Kayan aski na zamani maimakon Asake da maqera ke samarwa, kamar kilifofi masu amfani da wutar lantarki ko batura da sauransu.
- Wuqake na zamani da ake samarwa maimakon waxanda Maqera ke Samarwa ga masu sana'ar Fawada Jima da Sassaqa da sauransu.

- Injinan walda masu amfani da gas ko wutar lantarki domin haxawa ko raba qarfe, maimakon a da wannan aikin sai an dangana da maqeri.

**5.2. Kayan Amfanin a Daji**

- Tarakata da injina domin huxa ko aikin noma maimakon Galmar shanu ko ta hannu da maqera ke samarwa.
- Injina da na'urorin sare itatuwa maimakon Gatura da maqera ke qerawa.
- Bindigogi na zamani domin farauta a daji.

**5.3 Kayan Kare Kai**

- Qyaware- waxanda zamani ya kawo, maimakon wanda Maqera ke qerawa a cikin maqerunsu, wanda ada ba haka suke ba.
- Makamai- canjin da aka samu a vangaran makamai sun haxa da bindigogi da takubba na kamfani da masu na yaqi da jiragen yaqi da wuqaqe na zamani da dai sauransu.

**5.4 Kayan Gudanar da Sana'ar qira**

Hausawa na cewa xaki ba ya ta shi ya bar ragaya, wannan haka yake, kayan gudanar da sana'ar qira suma sun sami canje-canje, kaxan daga ciki akwai-

- Zuga-zugi-wannan an maye gurbinsa da xanwani, ma'ana wani gare ne na babur ake sa wa roba a rinqa wanawa yana bada iska kamar yadda zuga-zugi ke bada iska.
- Madoshi- ana amfani da injin na zamani yanzu domin huda qota ko wuqa ko wani makami wanda ada sai an yi amfani da madoshi a maqera.
- Makoxi/mawashin Qarfe-zamani ya kawo canji wajen samar da inji na koxa qarfe mai makon ada maqeri ke sa shi a wuta ya yi ja, sannan a fitar a sa zarto na maqera wasa shi. (Hira da Maqera).
- Almakashi domin datsa ko yanka qarfe a da, yanzu kuwa ana amfani da injina na zamani a yanka qarfe, wani lokaci ma gyararre za sawo asarrafa.
- Walda ta amfani da wutar lantarki don sarrafa qarfe maimakon a da sai an kai ga maqeri. Da dai suransu.

**6.0 Kammalawa**

Kamar yadda masu iya magana ke cewa “Komai nisan dare gari zai waye” kuma “komi ya yi farko zai yi qarshe” Wannan takarda ta yi magana ne a kan irin canjin da ake samu a cikin sana'o'in Hausawa,inda takardar ta karkata akalarta a kan sana'ar Qira domin fito da irin canjin da ta samu a dalilai canje-canje na yau da kullum a cikin al'umma.Har ila yau, takardar ta kawo irin kayayyakin da sana'ar ke samarwa a cikin al'umma da yadda ake gudanar da ita a jiya da kuma yau, domin qira tana cikin manyan sana'o'i na duniya. Galibin aikace-aikace, ba su yiwu wa sai da taimakonta. Amfaninta ba ya lissafuwa sai dai a faxi kaxan. Ga kayan noma, ga na fawa, da jima da sassaqa da aski, da sauransu da yawa. Duk waxannan, sai maqeri ya sa hannu sa'an nan su yiwu. Ko tuwon da ka ke ci kullum, tuna sai da aka qera fartanya, kana aka noma hatsin. Kai kowane irin aiki dai ko shi kansa ba a yinsa da qarfe, in ka bibiya, can farkonsa ko qarshensa, za ka samu da ruwan maqeri a ciki.

## Manazarta


Ado, A. (2014). *Sana'ar Gardancin Hausawa: Asalinta da Yadda Take da Yadda Ake Yin ta Qasar Hausa.*Al'adab Cairo Egypt.

Alhassan, H. Da wasu, (1982). *Zaman Hausawa.* (Babu Maxaba'a).

Aliyu, A. (2010) "Kamanci da Bambancin Tsakanin Hausar Katsina da Maraxi" Bincike kan Sana'ar Kira" B.A Hausa. Umaru Musa Yar'adua Katsina.

Brob, M. Da Baba, A.T. (1996). *Kamus na Sana'o'in Hausa* (Westaafrikansitu Studies vol x) Koln.

Xan'Iya, M.A. (2006). *Tasirin Kimiya da Qere-qeran Zamani Akan Sana'o'in Hausawa na Gargajiya.* Kano Kabs Print Services Nigeria.

Galadanci, M.K.M, da wasu (1992). *Hausa Dan Qananan Makarantun Sakandere.* DE-ATMAN Press Litd.

Garba, C. Y. (1991). *Sana'o'in Gargajiya a Qasar Hausa*. Spectrum Books Limited.

Koko, H.S. (2011). *Hausa Cikin Hausa*. Sashen Nazarin Harsunan Nijeria, Kwalejin Ilimi ta Shehu Shagari Sakkwato.

Madabo, M. H. (1976). *Ciniki da Sana'o'i a Qasar Hausa* N.N.P.C. Zaria.

Maxauci, I. da wasu (1968). *Hausa Customs.* N.N.P.C. Zaria.

Rimmer, E.M. da Wasu, (1966). *Zaman Mutum da sana'arsa* N.N.P.C. Zaria.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci Da Muhimmamcinsa Ga Rayuwar Hausawa*. M.A. Najiu Professional Printers No. 3 Kenya Road Malali Kaduna.

Yahaya, I. Y. da Xangambo, A. (1986) *Jagoran Nazarin Hausa* N.N.P.C. Zaria.

Hira da Maqera (10 Yuni, 2015) A Garin Qarqarqu Cikin Qaramar Hukumar Ingawa, Jihar Katsina.

Lacca Note. NLH 8324 Nigerian Languages Dept. Umaru Musa 'Yar'adua University Katsina. Oktober,2015.